# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na shida: Kariya da laifi

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya tace: Ludger Schadomsky da Maja Braun
Wanda ya fassara: Yusuf Idris

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| 'Yar jarida: | 'yar shekara 25 |
| Mr. Madu: | ɗan shekara 54 |
| Insifeto: | ɗan shekara 40 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da warhaka da kuma sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” a kan wasan ƙwallon ƙafa. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda abokantaka tsakanin Shehu da Zakari ta yi tsamari, saboda munafuntar da Shehu ya yi wa Zakari na zagayawa ya je inda za a yi gasar zaɓen ’yan wasa. Shi kuwa mahaifin John, wato Honourable Gambo, ya nan yana shirya wata ƙulleleniya, a yayin da shi kuma Metogba, ya buƙaci a ƙara shirya mishi wani taron ’yan jaridu. A ƙarshen shirin kuma, kun ji irin halin da Anti Lily ta shiga a gaban Safina da Zakari. Yanzu sai a kasance da mu domin jin yadda shirin zai ci gaba a yau.

**Fitowa ta 1: A garin Gabas**

Honourable Gambo, Shehu

**HON. GAMBO:** Kai! Kai yaro! E, kai! Zo nan! Kai ne Shehu?

**SHEHU:** Ni? A’a, amma zan iya nemo maka shi.

**HON. GAMBO:** Kai! Kar ka mai da ni sakarai mana! Na san kai ne Shehu. Kana so ka samu kuɗi cikin sauƙi, ko a’a ?

**SHEHU:** Kuɗi? E, ina so! Amma me kake so in yi maka, Malam?

**HON. GAMBO:** Shigo! Shigo cikin mota! Amma ka goggoge jikinka tukuna.

**MAI GABATARWA:**

Me kuma Honourable Gambo yake nema daga yaro kamar Shehu? Ba wanda zai iya sani, amma wani lokaci wasu mutane, musamman ma masu muƙami, za su bi duk irin hanyar da za su bi don su sami biyan buƙatunsu. Wan shekare kuma Safina ta farka da wuri, tana ta aikace-aikacen gida saboda ta samu ta je wurin gasar da wuri. Amma za ta je kuwa?

**Fitowa ta 2: A gidan Anti Lily**

Safina, Anti Lily

**SAFINA:** Anti Lily! Anti! Na gama abinci, na share gidan, kuma na yi wanke-wanke da sauran abubuwa. Sai na dawo.

**ANTI LILY:** Ke tsaya! Me kike nufi da sai kin dawo... Wayyo Allah! Kaina kamar zai fashe!

**SAFINA:** Ina ganin jiya kin sha wani abu ne mai ƙarfi. Sai da muka riƙe ki, muka shigar da ke gida.

**ANTI LILY:** Ku? Su wane ne ku? Safina, mene ne? A'a! Wa ya fasa min taga? Sannan ke kuma kina ina haka ya faru? Wani abu ya ɓace?

**SAFINA:** Ba abin da ya ɓace, Anti. Game da tagar kuma, bayanin da nake so in yi miki ke nan dama kafin in tafi. Jiya kafin ki... maganar tagar…wani yaro ne ya fasa ta. Yaron da ya tamaike ni muka ɗora ki a kan gado.

**ANTI LILY:** Yauwa, yanzu na tuna! Safina har kin fara kawo mini yara gidana ne?

**SAFINA:** A'a! Ko kaɗan! Zaks abokina ne kawai kuma mun haɗu da shi ne...

**ANTI LILY:** Me kika ce?

**SAFINA:** Cewa na yi Zakari, wani ɗan layi, shi ne yaron da ya fasa miki taga kuma daga baya, sai kamar dai...muka yi bugun daga kai sai mai tsaron gida, sannan kuma...

**ANTI LILY:** Zakari! Ɗan zaman banza a kan titi kika kawo min ɗan iska gidana? Ikon Allah! Kin buga ƙwallon ƙafa?

**SAFINA:** Amma ai yana da kirki, sannan ma ya ce ai ya san ki. Ya ce kina kyautata mishi ko da yaushe.

**ANTI LILY:** Fita! Fita, fita! Kwashe kayanki ki bar min gidana! Fita! Ki fice na ce!

**SAFINA:** Amma wane laifi na yi, Anti?

**ANTI LILY:** Kin karya dokata, kin kunyatar da ni, kuma ke kika jawo wa kanki wannan. Ya kamata a ce kin saurari abin da nake gaya miki. Maza ki fice, ki bar mini gidana!

**SAFINA:** Ina za ni, Anti? Ban san kowa ba a garin nan.

**ANTI LILY:** Babu abin da ya dame ni.

**SAFINA:** Ki yi haƙuri! Anti Lily, don Allah ki yi haƙuri!

**MAI GABATARWA:**
Allah sarki Safina! An ƙyale ta da 'yar jakarta a hannunta. Ina za ta daga nan? Za ta koma ƙauye ne wurin iyayenta? Ko kuwa wurin Zaks? Za ta so ta ci gaba da zuwa wurin gasar zaɓen 'yan wasan kuwa? Za ta iya jurewa hatsarurrukan titunan birnin Gabas kuwa? Irin waɗannan tambayoyin ne suka dabaibaye mata zuciya. A halin da ake ciki kuma, har Metogba ya riga ya isa filin wasa tare da Mr. Madu, shugaban ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasa, suna shirye-shiryen gudanar da taron 'yan jaridu da kuma ci gaba da gudanar da gasar, wanda ta shiga kwanaki na biyu.

**Fitowa ta 3: Taron 'Yan jaridu a babban filin wasa**

John, Metogba, Shehu, Mr. Madu

**METOGBA:** Mene ne wannan? Me ya sa mutane a ƙasar nan ba sa daraja lokaci ne? Me ya sa koyaushe sai su riƙa zuwa wuri a makare, Mr. …mmm… yaya ma sunan? Madu ko?

**MR. MADU:** Metogba, ka san cewa talauci ya yi wa mutane yawa a nan, kuma yawancinsu sun dogara ne a kan shiga motar haya ko kuma su taka da ƙafa.

**METOGBA:** Dakata, Malam! Ba a haife ni da arziki ba, amma an koya min sanin muhimmancin tsai da lokaci. Muna ɓata lokaci mai yawa, wanda za mu iya yin amfani da shi wajen yin abubuwa masu amfani. Ina nufin 'yan jaridu, yaya za a yi a ce ɗan jarida yana makara?

**MR. MADU:** Har yanzu ni ban fahimci dalilin da ya sa ka ƙara kiran taron 'yan jaridu ba. Jama'a sai su fara tunanin cewa kana so ka yi takara ne. Yauwa, ga ta tana shigowa.

**'YAR JARIDA:** Sannunku dai, sannunku dai! Don Allah ku yi haƙuri na ɗan makara. Muna iya farawa?

**METOGBA:** Ina 'yan gidan talabijin ɗin da masu ɗaukar hoto da sauransu?

**'YAR JARIDA:** Ban sani ba. Ina ganin kamar ka ɓata wa wasu rai ne. Idan ka shirya zan kunna rekodata.

**METOGBA:** Na shirya.

**'YAR JARIDA:** Yanzu haka muna babban filin wasa ne, inda ake gudanar da zaɓen 'yan wasa inda kuma sanannen ɗan wasan nan na

nahiyar Afrika, Metogba, zai yi wa 'yan jaridu ƙarin haske game da yadda gasar take tafiya. To yanzu Metogba, yaya gasar take tafiya da 'yan wasan?

**METOGBA:** Na kira wannan taron 'yan jaridun ne saboda abu ɗaya. Don in yi roƙo. Ina roƙon dukkan jama'ar ƙasar nan, 'yan siyasa, 'yan kasuwa, shugabannin addinai, ƙungiyoyin 'yan ta'adda, da shugabanninsu, jami'an gwamnati da masu son wasan ƙwallon ƙafa da cewa, don Allah a bar yaran nan su samu damar cim ma burin da suka sa a gaba. Yau, da a ce ban samu irin wannan damar ba na yin wasan ƙwallon ƙafa, da ba zan kasance a wurin nan ba. Saboda haka, duk inda kake, kuma ka ji wannan labarin a cikin rediyo, ina buƙatar waɗanda suke da yara a ƙarƙashinsu, maza ko mata, da suka mai da su sojoji, ma'aikatan gona, ko 'yan talla, don Allah ku tura su makaranta. Waɗanda kuma suke da sha'awar su zo nan inda muke gudanar da wannan gasa, to ku ƙyale su su zo. Na gode.

**'YAR JARIDA:** Ina fata kun saurari wannan roƙo na gaskiya daga bakin Metogba. To Metogba, wataƙila akwai wasu yaran da za su so su halarci wannan wuri, amma sai su rika tunanin wane irin riba za su samu idan suka zo?

**METOGBA:** Da yawa. Ba ƙwarewa a kan wasan ƙwallon ƙafa kawai za mu koyar a nan ba. Za mu koyi abubuwa masu muhimmanci da suka shafi rayuwarmu ta yau da kullum. Za ku koyi abubuwa a kan aiki tare, da kuma gudanar da rayuwa mai inganci. Ɗan wasan da ya fi kowanne ƙwarewa a gasar, zai samu kwanturagi da ƙungiyar ƙwallon ƙafar da nake yiwa wasa ta Turai duk lokacin da ya cika shekaru goma sha takwas. Kuma ina tunatar da ku cewa, duk 'yan wasan da na zaɓa a nan, za su zagaya ƙasashen Turai inda za su buga wasannin

sa da zumunci, kuma ba za ku san waɗanda za su kalle su ba.

**'YAR JARIDA:** To kun dai ji daga bakin mai abin da kanshi, wato Metogba. Ni ce taku Zainabu Abu, daga sashen Hausa na rediyon birnin Gabas.

**METOGBA:** Na gode, sai an jima. To kowa ya shirya. Kun dai san abin da muke yi, a zagaya sau biyar, sannan mu haɗu tsakiyar fili in mun gama. Ina Zakari ne da Safina? Shehu, ka san inda suke?

**SHEHU:** A'a ban gan su ba, *Coach*.

**JOHN :** To yaya za mu yi ke nan, *Coach*? In ba su ai *team* ɗinmu bai cika ba.

**METOGBA:** Kar ka damu kanka da wannan yanzu, John. Oya! *Go, go go!* Kuna ina ne? Maza, maza, maza! *Come on, come on!* …

**MAI GABATARWA:**

Kungiyar ba ta kwarin gwiwa, kuma Metogba ya fahimci haka. Shi kanshi ya fafar jin jinin jikinshi a kan wasu abubuwa daga waje. Zai ci gaba da wannan harka ko kuwa zai bar ta ne kawai ya yi tafiyarsa? A yayin da Metogba yake juya yin waɗannan tambayoyin a zuciyarsa, sai ga Zaks da Safina suna shigowa filin wasan. Safina na rataye da jakarta.

**Fitowa ta 4: A babban filin wasa**

Insifeto, Zakari, Safina, Metogba

**SAFINA:** Ban san yadda zan gaya wa Metogba wannan abin ba. Jiya-jiyan nan fa kawai muka san shi.

**ZAKARI:** Ki ƙyale ni da wannan.

**METOGBA:** Ban san yadda kuka ɗauke ni ba, amma wannan ba gudu ba ne! Zaks, kai da Safina, zan yi magana da ba ku bayan mun gama *practise*. Kowa ya zo nan! Yanzu, wa zai iya gaya min, mene ne abubuwan da suke sa ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta yi ƙarfi?

**JOHN:** Kuɗi. Idan kana da kuɗi masu yawa, za ka iya sayen duk ɗan wasan da kake so.

**METOGBA:** Ba haka ba ne, John. Duk da cewa kuɗi na taka rawa sosai a harkar wasan ƙwallon ƙafa ta ƙwararru, amma ba gaskiya ba ne cewa ɗan wasan da ya fi kowanne tsada zai kawo maka nasara a ko da yaushe.

**ZAKARI:** *Team* mai kyau yana buƙatar 'yan wasa masu kyau, masu tare baya, da kuma masu kai hari.

**METOGBA:** Wannan ita ce amsa mai kyau! To, yau za mu yi *training* ne a kan waɗannan ɓangarori guda biyu. Ku tuna cewa, wasa tare na taka rawar gani a kowace ƙungiyar ƙwallon ƙafa. Dole ne 'yan baya su taimaki masu wasa a tsakiyar fili, masu wasa a tsakiya kuma su taimaki masu neman cin ƙwallo. Saboda haka, mu je! … Me nake gani haka! Mene ne kuma? Yanzu an zo a kama ni ne? Saboda me? Na jawo tashin hankali a wurin gudanar da gasa?

**INSIFETO:** A cikinku nan wane ne Zakari?

**METOGBA:** *Officer*, me ya faru?

**ZAKARI:** Ni… Ni ne Zakari.

**INSIFETO:** Mun kama ka, saboda ka fasa shagon "Shah Electronics". Saboda haka sai ka biyo mu.

**ZAKARI:** Mene!?

**MAI GABATARWA:**

Ba Zaks kaɗai ba ne abubuwan da ke faruwa suka ba shi mamaki, Metogba, da sauran 'yan wasa sun kasa magana. Da gaske ne abin da ake zargin Zakari da shi? Yanzu me zai samu Zaks, da ƙungiyar, da Safina, wadda ta yarda da Zakari? Tambayoyi da yawa, kuma amsoshinsu za su kasance ne a cikin shirinmu na gaba. Ana iya sake sauraron wannan shirin ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/Ibe.